# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Tuntuɓar juna tsakanin addinai: Haɗin kan mutanen Sodangi
## Kashi na huɗu: A ƙarƙashin gadar Sodangi

Wanda ya rubuta: Romie Singh
Wanda ya tace: Katrin Ogunsade, Naïma Guira
Wanda ya fassara: Ɗanlami Bala Gwammaja

**'Yan Wasa:**

Dauda: ɗan shekara 17
Layla: 'yar shekara 16
Shugabar makaranta (Madam Titi): 'yar shekara 48
Saima: 'yar shekara 16
Hassan: ɗan shekara 12, ɗan'uwan Layla

**MAI GABATARWA:**

Jama'a, barkanmu da sake saduwa da ku a cikin wani sabon shirinmu na "Ji Ka Karu" a kan wasan kwaikwayon nan na "Haɗin kan mutanen Sodangi", wanda aka shirya a kan yadda addini da siyasa suka zama tarnaƙi a tsakanin wasu al'ummomi biyu da kuma wasu gidaje biyu. A wannan kashin mai suna "A ƙarƙashin gadar Sodangi", shugabannin ɗaliban nan, Dauda Dambele da kuma Layla Umar, sun fahimci irin sauyin da wannan sabuwar Kungiyar Muhawarar nan za ta kawo ga rayuwar ɗaliban Kwalejin Zumunta.

**Fitowa ta 1: A Kwalejin Zumunta**

Shugabar makaranta

**SHUGABAR MAKARANTA:** Madalla da irin wannan waƙa mai daɗi da kuka rera mana. Ku ɗalibaina ne! Don haka ina so in ƙarfafa muku gwiwa, ku zama masu ƙoƙari. Ku sani cewa, kowa ya yi da kyau, to fa zai ga da kyau. To amma kar mu ce za mu yi wani aiki don neman sakamako kawai, ko don samun wata ɗaukaka a Lahira, ko don samun wani babban muƙami, ko kuma don samun irin motocin nan na zamani, a'a! Duk abin da za mu yi, mu dage mu yi shi da gaske. Sakamakon shi ne mu ji cewa mun yi iya bakin ƙoƙarinmu! Kuma hakan zai fi kyau idan mun ji cewa aikin namu ba mu kaɗai ya amfana wa ba, a'a har ma da sauran jama'a. Wannan ita ce babbar manufar Kwalejin Zumunta. Yanzu sai kowa ya tafi aji, Allah kuma ya ba da sa'a.

**Fitowa ta 2: A Kwalejin Zumunta**

Dauda, Layla

**LAYLA:** Dauda, kana lafiya?

**DAUDA:** Au ni? Lafiya lau, Layla.

**LAYLA:** Yaya na gan ka haka-haka ne yau? Da ma na zo ne na faɗa maka cewa shugabar makaranta tana son mu haɗu da ƙarfe goma sha biyu a ɗakin karatu. Tana so ne mu tattauna a kan Kungiyar Muhawara, saboda za a fara zama ranar Alhamis.

**DAUDA:** Abin ya yi. Na san Layla za ki ga kamar na ɗan canza miki yau, to ba haka ba ne. Matsalar kawun nan nawa ne dai ta taso. Uhmm… zo mu fita waje mana mu yi wata 'yar shawara, ko kuma ma dai, bari sai an jima.

**LAYLA:** Na ga abin naka ba na wasa ba ne. In ce ko dai ba ɓaci ta yi ba?

**DAUDA:** Ni ba na son zance yanzu. To, mu haɗu mana a ƙarƙashin gadar Sodangi idan an tashi daga makaranta.

**LAYLA:** Gaskiya ƙanena na zuwa da ƙarfe uku ya raka ni gida.

**DAUDA:** Af, to idan ba zai damu ba, ni ma sai na raka ki. Yaya kika gani?

**LAYLA:** Shi ke nan. Ai ka fi ƙarfin haka. Ai ba kome wallahi!

**DAUDA:** Kai! Na ji daɗi! To, sai mun haɗu a ɗakin karatun da ƙarfe sha biyun.

**LAYLA:** To, sai na gan ka!

**Fitowa ta 3: A filin wasa**

Saima, Layla

**SAIMA:** Anya Layla, ni fa na ga yau fuskar nan taki sai annuri take?

**LAYLA:** Kai, Saima! Ke fa kin cika sa ido!

**SAIMA:** Aha! Ni fa na san akwai wani abu. Ni kuwa bari in canka…Tafida Magaji ne ya ce zai zo ku fita?

**LAYLA:** Me kika ce? Don Allah ki bar wannan zancen!

**SAIMA:** To, tsaya, bari in sake canka…Ina jin Dauda Dambele ne!

**LAYLA:** Don Allah Saima ki bari haka! Aikin makaranta ne fa kawai ya haɗa mu. Kuma in ban da abinki, yaya kike sa ran zan yi aikina na shugabar ɗalibai, idan duk abin da kika ga mun yi sai kin yanke hukunci a kai?

**SAIMA:** Wato ma duk abin da na ga kun yi ne ma. Lalle abin na yi ne!

**LAYLA:** Yaya kike lauya mini duk abin da na faɗa? Kin ga dakata, mu bar wannan maganar haka. Kin ga don Allah ɗaure min hijabina ta baya, don kar idan muna gudu gashina ya dinga zubo min a fuskata.

**SAIMA:** Layla ta shiga kogin soyayya, Layla ta shiga kogin soyayya!

**LAYLA:** Wash, kina ja min gashi!

**SAIMA:** Sannu, yi haƙuri!

**LAYLA:** Mu ɗan motsa jikinmu mana kafin mu fara gudu.

**SAIMA:** To, ni dai ina jin daidai na canka da na ce Tafida ne a ciki. Don kuwa na lura shi yake ta binki duk inda kika sa ƙafa!

**LAYLA da SAIMA:** *One, two, three. One, two, three. …*

**Fitowa ta 4: A ɗakin karatu**

Shugabar makaranta, Dauda, Layla

**SHUGABAR MAKARANTA:** Au, ashe ku tuni ma kun zo. To yanzu me kuka yi a wancan satin?

**DAUDA da LAYLA:** Ai ba wata matsala, Malama.

**LAYLA:** Abin da muka yi shi ne, mun nemi yawancin ɗalibai da su ba mu batutuwan da suke son su tattauna a kai, a lokacin da Kungiyarmu ta Muhwara za ta fara aiki.

**DAUDA:** Mun kuma tattauna da ɗalibai 'yan aji ɗaya da 'yan aji biyu-mazansu da matansu.

**SHUGABAR MAKARANTA:** Daga nan fa?

**DAUDA:** To, mun fahimci cewa batu na farko da aka fi ambata shi ne, batun auren mace fiye da ɗaya.

**SHUGABAR MAKARANTA:** Hmm, ba mamaki. Ai wannan zancen ake ta yi a gari, tun lokacin da aka samu labarin ministanmu na lafiya ya auri matarsa ta biyar!

**LAYLA:** Gaskiya, wannan shi ne dalili. To, amma shi yana ganin burgewa ya yi, a wannan zamanin da ake ta fama da cutar HIV/AIDS?

**SHUGABAR MAKARANTA:** Lalle kam, wannan ma wata hujja ce da ta sa ya kamata a tattauna a kan batun.

**LAYLA:** Sannan kuma batu na biyu da aka fi ambata shi ne: Anya kuwa Kwalejin Zumunta tana yin iyakar iyawarta don ganin ta ƙarfafa wa mata gwiwa don su rungumi harkokin wasanni?

**SHUGABAR MAKARANTA:** To, ina jin wannan batun mata ne suka kawo shi.

**LAYLA:** Kwarai kuwa. Kin san fa cewa 'yan matan Musulmi dole ne sai sun rufe jikinsu da hijabi kamar yadda addininsu ya umarta. Amma kuma malamin da yake kula da wasanni ya ce ba zai ƙara yarda a sa hijabi, ko riguna masu dogon hannu ba, wai saboda ba su dace da irin kayan da ake wasannin da su ba.

**DAUDA:** Ya kamata ku fa sani cewa wannan mataki ne da Kwamitin Wasanni na Makarantun wannan yanki ya ɗauka.

**LAYLA:** A haƙiƙanin gaskiya ma, ko su samarin Musulmi ba a yarda su dinga fito da cinyoyinsu da kuma damatsansu waje ba. Amma kuma abin ya fi tsanani a kan mata, saboda su dole ne su rufe kawunansu. Hakan kuwa ya sa ana yi ba su.

**SHUGABAR MAKARANTA:** Hmm… To, lalle fa akwai buƙatar mu duba wannan doka don mu ga yadda za mu tattauna da Kwamitin Wasanni a kanta.

**LAYLA:** Madam, ni ina ganin wataƙila batun da ya kamata mu kawo shi ne: Shin ko ya dace a sassauta dokokin kayan wasanni, don a ƙarfafa wa Musulmi shiga cikin harkokin wasanni?

**SHUGABAR MAKARANTA:** Haka ne. Bari zan gabatar da wannan matsala a gaban Hukumar Makaranta. A yanzu dai na san kun sami ƙwararan batutuwan da za ku yi muhawara a kai! Akwai wata Gasar Muhawara ta shiyya-shiyya da za a gabatar a garin Sodangi mai taken “Bayyana ra’ayinka kai tsaye”. Ya kamata mu mayar da hankalinmu zuwa fuskantar wannan gasa. Yanzu bari in bar ku don ku ci gaba da shirye-shiryenku na buɗe Kungiyar Muhawara ta farko ta Kwalejin Zumunta. Allah ya ba da sa’a!

**TAFIDA da LAYLA:** Amin, mun gode. Sai an jima, Malama.

**DAUDA:** Kai, ni ma fa ya kamata na tafi. Za mu haɗu da ƙarfe uku a babbar ƙofar shiga ɗakin karatu. Sai na gan ki! Da ma kuwa ina so na ga Hassan.

**LAYLA:** Hmm… Abin ya yi!

**Fitowa ta 5: A babbar ƙofar shiga makaranta**

Layla, Dauda, Hassan

**LAYLA:** Hassan, wannan shi ne Dauda, shugaban ɗalibai na makarantarmu.

**DAUDA:** Hassan, barka da ganinka.

**HASSAN:** Layla, zo mu tafi mana!

**LAYLA:** Kai Hassan, kar ka yi haka mana. So nake ni da Dauda mu ɗan yi hira ta rabin awa.

**HASSAN:** Me kika ce? Ku kaɗai?

**DAUDA:** Kai Hassan, ba fa daɗewa za mu yi ba. Na san ba za ka damu ba idan na raka 'yar'uwarka gida nan da awa ɗaya.

**HASSAN:** Ni ma sai na bi ku.

**LAYLA:** Kai Hassan, don Allah ka tafi gida! Idan mun gama zan taho.

**HASSAN**: Kin san fa addinimu ya haramta haka. Sai na faɗa wa Baba idan ya dawo.

**DAUDA:** Ina fata dai ba fushi yake da ni ba?

**LAYLA:** Yana yi mana, ka san 'yan kwanakin nan fushi yake da kowa ma. Gaskiya Dauda, ka san fa ba zan daɗe ba. Babana ba ya nan, kuma bai kamata na bar Hassan shi kaɗai na wani tsawon lokaci ba. Ka san shi har yanzu bai wattsake daga mutuwar mamanmu ba.

**Fitowa ta 6: A gidan Malam Isma'ila**

Hassan

**HASSAN:** Wayyo Mama! Me ya sa kika tafi kika bar ni? Ina ma muna tare da ke! Manyanmu a makaranta suna gaya min cewa wata rana za mu haɗu da ke a aljanna, idan ina yaƙar kafirai. Su Kiristocin nan ba ƙaunarmu suke ba. Ba sa ƙaunar gina masallatan da muke yi. Allah Sarki, Mama! Ina ma ni na mutu!

**Fitowa ta 7: A ƙarƙashin gadar Sodangi**

Dauda, Layla

**DAUDA:** Biyo ta matattakalan nan. Yauwa! Gaskiya ƙarƙashin gadar nan da sanyi yake. Ungo kwat ɗina, zauna a kai.

**LAYLA:** Na gode, Dauda.

**DAUDA:** Layla, kin san dai, uhmm... cewa da gidanmu da naku ba wani shiri suke ba!

**LAYLA:** Me kake nufi?

**DAUDA:** Uhmm... A kan dai kawun nan nawa ne. Kin san shi ba ya ƙaunar ya gan ni da ke bayan an tashi daga makaranta.

**LAYLA:** To, me ya sa kawun naka ba ya ƙaunata?

**DAUDA:** Ba wai ke ce ba ya ƙauna ba. Bari in gaya miki, tun asali da ma da zuriyar Umar da ta Dambele abokan adawa ne. Ni babana ya gaya min cewa abin a kan wani fili ne da kuke son gina masallaci.

**LAYLA:** A'a! Kuna dai son ku gina coci a ciki.

**DAUDA:** To, kin ga fa inda matsalar take. Amma dole mu nemo hanyar warware ta.

**LAYLA:** Gaskiya ne. To, dole sai mu bar hukumar raya wannan yankin ta yanke hukunci.

**DAUDA:** Haƙiƙa! Abin da ya kamata mu dinga faɗa ke nan. Ina so na...uhm...kome ya rikice min! Abin da nake son na ce shi ne…

**LAYLA:** Ina jinka!

**DAUDA:** Uhm… Don Allah kar ki bari wannan matsala ta shiga tsakaninmu. Ni me ƙaunarki ne Layla. Yanzu fa mun kai shekara muna tare. Amma kuma ga shi...

**LAYLA:** Ina jin na san abin da kake son ka faɗa. Ni ma haka Dauda, ina son dangantakarmu ta fi ta da.

**DAUDA:** Layla, da gaske kike? To, amma tsaya! Idan kuma iyayenmu suka ƙi amincewa fa?

**MAI GABATARWA:**

Wannan shi ne ƙarshen shirinmu na "Ji Ka Karu" a yau. Dauda da Layla dai sun yanke shawarar shawo kan saɓanin da ke tsakanin iyayensu, sai dai kuma abin ya wuce yadda suke tunani. Sai ku biyo mu a kashi na biyar na wannan shiri namu na "Haɗin kan mutanen Sodangi" domin jin yadda za a ƙaddamar da Kungiyar Muhawara da aka kafa a Kwalejin Zumunta. Sannan kuma za ku ji wani labari mai sosa zuciya wanda zai kawo ruɗani a cikin wannan sabuwar soyayya da aka fara. Idan kuna buƙatar sake sauraron wannan shiri ko kuma aiko da tsokaci, kuna iya tuntuɓarmu ta adireshinmu na yanar gizo, wato www.dw-world.de/lbe.